# Ya Manzon Allah, waninmu ya iya kwanciya da janaba? sai yace: E, zai iya, amma in yayi alwala.

Daga Abdullahi Dan Umar Allah ya yarda dasu Umar Dan Khaddab Allah ya yarda da shi yace: [Ya Manzon Allah, waninmu zai iya kwanciya da janaba? sai yace: E, zai iya, amma in yayi alwala

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

An tambayi Umar Dan Khaddab -Allah ya yarda da shi- ya tambayi Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi: Idan janaba ta sami wani tun farkon dare ta hanyar saduwa da iyali ko mafarki, shi zai iya kwanciya bacci a haka? sai Mai tsira da amincin Allah ya basu damar yin haka amma idan anyi alwalla irin ta salla.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee